# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da



# Dan Sarki Ya zama Makiyayi


Wanda ya Rubuta: Edward Hughes

Mai Zane: M. Maillot; Lazarus
Alastair Paterson

Mai niyyan daukan nauyi: E. Frischbutter; Sarah S.



Fassarawa: Bible Society Nigeria

Wanda ya Wallafa: Bible for Children
www.M1914.org



©2024 Bible for Children, Inc.

Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan
har ba zaku sayar da shi.






Wata rana Musa ya ga wani mutumin Masar yana dukan wani bawa mutumin Ibriniyawa. Ko da yake an girmar da Musa an kuma ilmantar da shi a matsayin dan sarki a gidan sarki na Firauna, shi ma mutumin Ibriniyawa ne.

Sai ya taimaki bawan.


Yana waiwaiya domin ya tabbatar babu wani wanda yake ganin shi, sai Musa ya kai wa mai lura da bayi hari. A cikin fadan da ya bi, Musa ya kashe mutumin Masar. Da sauri-sauri, sai ya binne jikinsa.
3


Washegari, Musa ya ga mutanen Ibriniyawa guda biyu suna fada. Sai ya yi kokari ya raba su. Daya ya ce “Ko za ka kashe ni kamar yadda ka kashe mutumin Masar ne?” Musa ya ji tsoro. Ashe kowa ya san abin da ya faru jiya. Firauna ya sani. Dole Musa ya gudu. Sai ya tafi wata kasa mai suna Midiyan.
4


Sa’ad da Musa yana hutawa a bakin rijiya, sai ‘yan mata bakwai na firisti na Midiyan suna cika tullunan ruwan domin tumakin babansu.
5


Wadansu makiyayi sun so su tura su a gefe. Musa ya tsare ya kuma taimaki yan matan.
6


“Yau kun dawo gida da sauri!” Rewuyel, baban ‘yan matan ya yi mamaki. Bayan da ‘yan matan suka bayana dalili, sai ya ce, “Ku kawo mutumin a nan.” Musa ya zauna da Rewuyel, wanda ake kuma kira Yetro.
Daga baya, sai Musa ya aure babbar ‘yar Rewuyel.
7


Can a Masar, Firauna ya mutu. Mutanen Allah, Ibriniyawa, har yanzu suna cikin bauta. Suna cikin tsanani a cikin wahalarsu.
Ina misalin addu’arsu domin neman taimakon Allah! Allah ya ji addu’o’insu.
8


Musa bai san da abin da yake faruwa ba, amma Allah ya shirya ya yi amfani da shi domin ya taimake Ibriniyawa masu bauta. Musa ya bar Masar Shekaru arba'in da suka riga suka wuce. Shi dama makiyayin tumakin Rewuyel ne.
Amma dole yana tunani a kan mutanensa a Masar.
9


Wata rana Musa ya hango wani dan daji yana konewa. Amma wutan bai cinye ciyawar ba. Musa ya fara neman sanin me ya sa.
10


Sa'ad da Musa yayi kusa, Allah ya kira shi daga dajin. "Musa!" "Ga ni nan," Musa ya ce. "Kada ka yi kusa sosai." Allah ya ce. "Cire takalmarka, gama inda kake tsaye kasa ce mai tsarki."
11


"Zan aike ka zuwa wurin Firauna domin ka fitar da mutanena daga Masar," Allah ya ce. Amma Musa ya ji tsoron zuwa.
12


Sai Allah ya nuna wa Musa ikonsa mai girma. Ya canja sandan Musa ya zama maciji.
13


Sa'ad da Musa ya dauki macijin a wutsiya, sai ya dawo sanda kuma. Allah ya sake ba da wani alama.
14

**“Saka hannunka a kirjinka,” Ya umarta. Musa ya yi haka. Hanunsa ya juya ya zama fari da kuturta.**



15

**Bayan da ya sake yin haka, sai hannunsa ya warke.**



16

**Har yanzu Musa bai yarda ba. “Ban iya magana sosai ba,” ya gaya wa Allah. Allah ya yi fushi. “Zan yi amfani da Haruna, dan’uwanka, ya yi magana duk abin da za ka fada masa,” Ya ce.**



17

**Musa ya koma zuwa wurin Yetro, ya kwashe kayansa ya tafi Masar.**



18

**Allah ya bi da Haruna dan’uwan Musa domin ya sadu da Musa a tuddai. Musa ya fada wa Haruna duka game da shirin Allah domin ya ‘yantar da mutanen Ibriniyawa daga Masarawa. Tare, suka kai labarin ga shugabanan Ibriniyawa. Sa’ad da Musa ya nuna alamun ga dattawan Ibriniyawa, sai suka sani Allah zai taimake su. Tare, suka sunkuyar da kawunansu suka yi sujada.**



19

**Cikin karfin hali, Musa da Haruna suka tafi wurin Firauna. “Allah ya ce, ’Ka bar mutane na su tafi’,” suka gaya masa.**



20

"Ba zan bar Isra'ila ta tafi ba," Firauna ya amsa. Ba zai yi biyayya ga Allah ba. Allah zai yi amfani da babban ikonsa ya canja tunanin Firauna.





**Dan Sarki Ya zama Makiyayi**

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Fitowa 2-5**

**"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130**



# KARSHE

10 60



**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**